# الإسلام - نبذة موجزة عن الإسلام

## (مجردة من الأدلة) (للجمعية)

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin ƙai.

# MUSULUNCI

## Taƙaitaccen saƙo game da Musulunci kamar yadda yazo cikin Al-Kur'ani da Sunnanr Annabi

(Kwafin da babu Nassoshi a cikin)[1]

Saƙo ne mai muhimmanci wanda ya ƙunshi taƙaitaccen bayani game da Musulunci, yana bayyana mafi muhimmancin tushensa da koyarwarsa da kyawawunsa wanda aka samosu daga tushe na asali shine Al-Kur'ani Mai girma da Sunnar Annabi, kuma saƙon an fuskantar dashi ne zuwa baki ɗayan baligai na musulmai da waɗanda ba musulmai ba, da yarukansu a kowane lokaci da wuri duk da sabanin yanayi da halaye.

1.Musulunci shi saƙon Allah ne zuwa ga mutane baki ɗayansu, shine saƙon Allah wanzajje.

2.Kuma Musulunci ba Addinin wasu kebantattun mutane bane ko jinsi a'a Addinin Allah ne ga mutane baki ɗayansu.

3.Musulunci shine saƙon Allah wanda yazo don cika saƙonnin Annabawa da Manzanni waɗanda suka

[1] Ana iya samun wani kwafin na wannan saƙon wanda yake haɗe da dalilai daga Al-Kur'ani da hadisan Annabi kan kowace Mas'ala a cikin sa, don karantawa jeka wannan shafin: https://islamhouse.com/ar/books/2830071.

gabata - amincin Allah ya tabbata a gare su- zuwa ga al'ummansu.

4. Annabawa - amincin Allah ya tabbata a gare su - Addininsu ɗaya ne kuma shari'unsu sun sha banban.

5. Musulunci yana kira - kamar yadda kowane Annabi yayi: Nuhu da Ibrahim da Musa da Sulaiman da Daud da Isa - amincin Allah ya tabbata agare su - zuwa ga imani cewa Ubangiji kaɗai Shine Allah Mahalicci Mai azirtawa, Mai rayawa, mai kashewa Mamallakin mulki, kuma Shine wanda Yake gudanar da al'amura, Shine Mai rangwami kuma Mai jin ƙai.

6: Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - Shine Mahalicci wanda Ya cancanci Ibada Shi kaɗai, kuma ba'a bautawa waninSa tare da shi.

7. Allah Shine Mahaliccin abinda muke iya ganinsa da abinda bama iya ganinsa, kuma duk wani abu da ba Shi ba to shi abin halitta ne daga cikin halittunSa, kuma Ya halicci sammai da ƙasa a cikin kwana Shidda.

8. Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - baShi da abokin tarayya a cikin mulkinSa da halittarSa ko jujjuya al'amuranSa, ko bautarSa.

9. Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - bai haifa ba kuma ba'a haifeShi ba kuma baShi da wani kini ko mai kamanceceniya da Shi.

10. Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - baYa sauka a cikin wani abu, kuma baya sajewa da jiki na halittarSa.

11. Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - Mai rangwame ne kuma Mai jin ƙai ne ga bayinSa; shi yasa Ya aiko Manzanni kuma Ya saukar da litattafai.

12. Allah Shi ne Ubangiji Mai jin ƙai Shi kaɗai wanda zai yi hisabi ga halittu a ranar al-Kiyama lokacin da Zai tashe su baki ɗayansu daga ƙaburburansu, sai Ya sakawa kowanne mutum da abinda yayi na alheri ko sharri, wanda yayi aiki na gari kuma yana mai imani to yana da ni'ama matabbaciya, kuma duk wanda ya kafirta yayi mummunan aiki to yana da azaba mai girma a lahira.

13. Allah - tsarki ya tabbaatr maSa Ya ɗaukaka - Ya halicci ɗan Adam daga turɓaya, kuma Ya sanya zurriyarsa tana yaɗuwa bayansa, mutane a asalisu daidai suke, babu fifko a tsakanin jinsi da jinsi ko wasu jama'a akan wasu jama'a sai da tsoron Allah.

14. Kowane yaro ana haifarsa ne akanturbar dai dai.

15. Kuma babu wani mutum da aka haifeshi mai kuskure ko mai gadan saɓon waninsa.

16.Kuma Manufa na halittar mutane ita ce bautar Allah Shi kaɗai.

17. Musilunci ya karrama mutum -maza da mata- kuma ya ɗauke masa baki ɗayan haƙƙoƙin sa, ya sanya shi abin tambaya akan sauran zaɓuɓɓukan sa, da ayyukansa da kuma tasarrufin sa, kuma ya ɗora masa

nauyin kowane irin aiki da zai cutar da kansa ko ya cutar da wasu daban.

18. kuma ya sanya namiji da mace daidai da daidai wajen ɗaukar alhakim aikinsu da kuma sakamako da bada lada.

19. Musulunci ya karrama mace, kuma ya sanya mata su zamanto abokan tafiyar maza, ya lazimtawa mijin ciyar da ita idan ya kasance yana da iko, saboda haka ya wajaba uba ya ciyar da ɗiyarsa, haka uwa akan ɗanta idan ya kasance baligine mai iko, haka mata akan mijinta.

20. Mutuwa ba ƙarewa bace ta har abada, a'a ita wata tafiya ce daga gidan aiki zuwa gidan sakamako, kuma mutuwa tana samun jiki da ruhi, mutuwar ruhi ita ce rabuwar ruhi daga jiki, sannan ya dawo zuwa jikin bayan tashin al-Kiyama, kuma ruhi baya tafiya zuwa wani jikin bayan mutuwa, kuma baya sake tsiruwa a wani jikin daban.

21. Musulunci yana kira ne zuwa imani da ginshiƙan imani manya, sune imani da Allah da mala'ikunSa, da imani da litattafan Allah kamar Al-taura da linjila da Zabura -kafin jirkita su- da al-Kur'ani, da kuma imani da dukkan annabawa da manzanni - amincin ya tabbata a gare su - kuma yayi imani da na ƙarshensu shi ne Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi a cikamakin Annabawa da manzanni, da imani da ranar Lahira, kuma mu san cewa rayuwar

duniya da ita ce ƙarshen rayuwa; da halitta da rayuwa sun zama wasa tsantsa, kuma da imani da hukuncin Allah da ƙaddara.

22. Annabawa ma'asumai ne - aminci ya tabbata a gare su - cikin abinda suka isar da shi daga Allah, kuma ma'asumai ne ga barin dukkanin abinda ya saɓawa hankali, ko kuma kyawawan ɗabi'u suka ƙyamace shi, kuma Annabawa an ɗora musu isar da umarnin Allah ga bayinSa, kuma annabawa basu da wani abu na abinda ya keɓanci Allantaka; a'a suma mutane ne kamar sauran mutane Allah Yayi musu wahayi da saƙonninSa.

23. Musulunci yana kira zuwa ga bautar Allah Shi kaɗai da ginshiƙan ibada manya, sune: Sallah wacce ita ce tsayuwa da ruku'u da sujjada da ambaton Allah da yabonSa da kuma addu'a, mutum yana sallatarta sau biyar a wuni, kuma a cikinta babu banbanci tsakanin mawadaci da talaka da shugaba da mabiyi a sahu ƙwara ɗaya a cikin sallah. Da kuma zakka wacce wani yanki ne kaɗan daga cikin dukiya - daidai da sharaɗɗa da kuma gwargwadon da Allah Ya ƙaddara,kuma tana wajaba ne a dukiyar mawadata kuma a bada ita ga talakawa da wasunsu, kuma sau ɗaya ce a shekara. Da kuma Azumi wanda shi ne: Kamewa daga abubuwan ci a yinin ramadan, yana horar da rai nufi da hakuri. sai hajji shine. Nufin ɗakin Allah a makka abar girmamawa sau ɗaya a rayuwa ga

wanda yake da iko, ma'anar wannan hajjin didaituwar kowa da kowa a cikin fuskantar mahalicci - tsarki ya tabbatar maSa, kuma banbance-banbance ya gushe da kuda kuma dangane-dangane.

24. Daga mafi girman abinda ibada ta keɓanta da shi a musulunci cewa yadda ake yinta da lokutanta da sharuɗɗanta Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - ne Ya shar'anta ta, kuma manzonSa - tsira da aimncin Allah su tabbata agare shi - ya isar da ita, babu wani mutum da yayi shigege a cikin ta ta hanyar ƙari ko ragi har zuwa wannan rana, dukkan waɗan nan manyan ibadun annabawa - amincin ya tabbata a gare su - sunyi kira zuwa garesu.

25, Manzon musulunci shi ne Muhammad ɗan Abdullahi daga cikin zuriyar annabi Isma'ila ɗan annabi Ibrahim - amincin Allah a garesu- an haife shi Makka a shekara ta 571 Miladiyya, kuma yai hijira zuwa Madina, kuma baiyi tarayya da mutanensa ba a Al-amuran bautar Gunki, sai dai shi ya kasance yana tarayya da su a Ayyukan kirki, kuma ya kasance kan kyawawan Halaye tun kafin a aiko shi, kuma Mutanensa sun kasance suna kiransa Amintacce, kuma Allah ya aiko shi yayin da ya cika Shekara Arba'in kuma Allah ya Qarfafe shi da da Ayoyi (Mu'ajizozi) Masu girma, kuma girmansu shi ne Al-qur'ani Mai girma, kuma shi ne mafi girman Ayoyin Annabawa, kuma shi ne Ayoyin Annabwa har zuwa yau ɗin nan,

kuma yayin da Allah ya cika wannan Addinin, kuma Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya isar da shi matuƙar isarwa sai ya yi wafati alhali shekarun manzon Allah suna sittin da uku, an binne shi a garin Madina - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, kuma manzon Allah Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - shine cika makin annabawa da manzanni Allah Ya aiko shi da shiriya da addini na gaskiya don ya fitar da mutane daga duhun bautar gumaka da kafirci da jahilci zuwa hasken kaɗaita Allah da imani, Allah Yayi masa shaida cewa Shi ne Ya aiko shi yana mai kira zuwa gare Shi da umarnin Sa.

26. Shari'ar musulunci wacce manzon Allah Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya zo da ita ita ce cika makin saƙonnin Allah da shari'un Ubangiji, kuma ita ce shari'ar cika, a cikinta akwai gyaruwar addinin mutane da duniyarsu, ita tana tsarewa a mataki na farko ga addinin mutane da jinanansu da dukiyoyinsu da hankulansu da zuriyarsu, kuma ta shafe kowa ce shari'a da ta gabaceta na daga shari'u, kamar yadda ta soke shari'un da suka gabata sashinsu da sashi..

27. Allah - tsarki ya tabbatar maSa Ya ɗaukaka - baya karɓar wani addini in ba musulunci ba wanda shine wanda manzo Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya zo da shi, kuma duk

wanda ya riƙi wanin musulunci addini to ba za'a karɓa daga gareshi ba.

28. Al-Kur'ani mai girma shi ne littafin da Allah Ya aikowa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata aagre shi - kuma shi ne zancen Ubangijin Talikai wanda Allah ya qure Mutum da Al-jann kan su zo da kwatankwacin sa, ko Sura kwatankawcinsa, kuma har yau qurewa bata qare ba, Kuma Al-qurani yana bada Amsar Muhimmai masu yawa da Muliyoyin Mutane suka gaza, Kuma Al-qurani Maigirma abun kiyayewa ne har zuwa yau xin nan da yaren larabci da ya sauka da shi, kuma ba'a rage ko harafi xaya ba, kuma yana nan a buge ana yaxa shi, Kuma littafi ne Maigirma Mai gajiyarwa wanda ya dace da a Karanta shi ko a karanta Fassararsa, Kamar yadda Sunnar manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - da koyarwarsa da tarihinsa ababan kiyayewa ne kuma ababan ruwaitowa ne daidai da tsanin jerin masu riwaya da aka yarda da su, kuma an bugasu da larabci wanda manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yayi magana da shi kuma an fassarasu da yaruka da yawa, kuma al-Kur'ani da sunnar manzon Allah su ne tushe ƙwara ɗaya na hukunce-hukuncen musulunci da shari'un sa, saboda ba'a ɗaukar musulunci daga aiyukan ɗaiɗaikun mutane da suke danganta kansu da musulunci; kawai

ana ɗauka ne daga Wahayin Allah a Al-Kur'ani mai girma da sunnar annabi.

29. Musulunci yana umarni da kyautatawa iyaye, koda kuwa sun kasance ba musulmai ba ne, kuma ya na wasiyya da 'ya'ya.

30. Musulunci yana umarni da adalci a cikin magana da aiki koda kuwa tare da abokan gaba ne.

31, Kuma Musulunci yana umarnini da kyautatawa halitta baki ɗaya, kuma yana kira zuwa kyawawan halaye, da kyawawan ayyuka.

32. Kuma musulunci yana umarni da kyawawan halaye kamar gaskiya, da sauke amana, da kamewa, da kunya, da gwarzantaka, da karamci, da taimakawa mabuƙaci, da kai gudun mawa ga wanda yake cikin wani hali, da ciyar da mai jin yinwa, da kyautata maƙwabtaka, da sadar da zumunci, da tausasawa dabbobi.

33. Musulunci ya halatta abubuwa masu daɗi na abin ci da abin sha, kuma yayi umarni da tsarkake zuciya da jiki da guri; saboda haka ya halatta aure, kamar yadda ya umarci annabawa - aminci ya tabbata a gare su - da hakan, saboda su suna umarni ne da dukkan abu mai kyau.

34. Musulunci ya haramta dukkan tushen haramun, kamar yiwa Allah shirka da kafirci, da bautar gumaka, da shaci faɗi ga Allah bada ilimi ba, da kashe 'ya'ya. da kashe ran da Allah Ya haramta, da ɓarna a

bayan ƙasa, da sihiri da alfasha ta fili da ta ɓoye, da zina da liwaɗi, kuma ya haramta riba, ya haramta cin mushe, da abinda aka yanka ga gumaka da dodanni, da cin naman alade, da sauran najasa da ƙazanta, kuma ya haramta cin dukiyar maraya, da tauye mudu da ma'auni, kuma ya haramta yanke zumunci, annabawa - aminci ya tabbata a gare su- baki ɗayan sun haɗu kan haramcin waɗan nan abubuwan.

35. Musulunci ya hana munanan halaye, kamar ƙarya, da ha'inci, da yaudara, da ha'inci, da danfara, da hassada, da mummunan kaidi, da sata, da zalunci, kuma ya na hana dukkan wasu munanan ɗabi'u.

36. Musulunci ya hana mu'amalolin kuɗi waɗanda a cikinsu akwai riba, ko cutarwa, ko garari, ko zalunci. ko algus, ko yana kaiwa zuwa ga masifu, ko cutarwar da zata game zamantakewa baki ɗaya ko ɗaiɗaikun mutane.

37. Musulunci ya zo da kiyaye hankuli, da haramta dukkan abinda zai ɓata shi kamar shan giya, kuma musulunci ya ɗaga darajar hankali ya sanya shi doron ɗora nauyi, ya 'yantashi daga dabaibayin tatsuniyoyi da bautar gumaka. Kuma a musulunci babu wasu ɓoyayyun abubuwa ko hukunce-hukuncen da suka keɓanci wasu mutane koma bayan wasu, dukkanin hukunce-hukuncensa da shari'unsa sunyi daidai da hankula ingantattu, kuma sunyi daidai da abinda adalci da hikima suka hukunta.

38. Addinan ɓata idan mabiyansu basu gamsu da abinda yake cikinsu ba na kwangaba kwanbaya, da al'amuran da hankali ba zai ɗauka ba, sai malaman mabiya addinin su ruɗi mabiyan da cewa ai addini sama yake da hankali, kuma cewa hankali bashi da wani fage a fahimtar addini da game fahimtarsa. Wanda musulunci kuwa ya ɗauki addini wani haske ne da yake haskawa hankali hanyarsa; Ma'abota addinan ƙarya suna son mutum ya bar hankalinsa ya bisu, musulunci kuwa yana son mutum ne da ya farkar da hankalinsa, don yasan haƙiƙanin al'amura kamar yadda suke.

39. Musulunci yana girmama ingantaccen ilimi, kuma yana kwaɗaitarwa kan binciken ilimi wanda yake babu son rai a cikinsa, kuma yana kira zuwa nazari da tunani a kawunanmu da halittun da suke kewaye da mu, sakamakon ilimi ingantacce don ilimi baya cin karo da musulunci.

40. Allah baYa karɓar aiki ko Ya bada lada akansa a lahira sai daga wanda yayi imani da Allah kuma ya biShi ya gasgata manzanninSa - aminci ya tabbata a gare su -, kuma Allah baYa karɓar ibadu sai abinda Ya shar'antashi, ta yaya mutum zai kafircewa Allah kuma ya ƙaunaci ladanSa? Allah baYa karɓar imanin wani daga mutane sai idan yayi imani da annabawa -aminci ya tabbata a gare su baki ɗaya -, kuma yayi imani da

saƙon (annabi) Muhammad - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -.

41. Lallai manufar dukkanin saƙonnin Allah shi ne: Addinin gaskiya ya ɗaukaka ɗan Adam, sai ya zama tsantsar bawan Allah Ubangijin talikai, kuma ya 'yanta shi daga bautar mutane ko wani abin duniya ko tatsunuyoyi, musulunci - kamar yadda kake gani - baya tsarkake mutane ya ɗagasu sama da matsayin su, kuma baya sanya su alloli ababan bauta.

42. Allah Ya shar'anta tuba a musulunci wanda shine: Komawar mutum zuwa ga Ubangijinsa, da barin zunubi, kuma musulunci yana rushe abinda ya gabaceshi na zunubai, kuma tuba yana wanke abinda ya gabace shi na zunubai, saboda haka babu wata buƙata ga mutum ya bayyanar da laifukansa a gaban mutane.

43. A cikin musulunci dangantaka tsakanin mutum da Allah kai tsaye ta ke, saboda haka baka buƙatar wani mutum da zai kasance tsani tsakaninka da Allah, saboda musulunci ya hana mu sanya mutane su zamanto Alloli ko masu tarayya da Allah cikin RububiyyarSa ko UluhiyyarSa..

44. A ƙarshen wannan saƙon muna tunsarwa cewa mutane duk da saɓanin zamaninsu da ƙabilunsu, da garuruwan su kai baki ɗayan duniyar mutane sun saɓa a wajen tunanisu da manufofin su, sun yi hannun riga wajen garuruwansu da ayyukan su, saboda haka suna

da buƙatar wani mai shiryarwa da zai ɗorasu kan turba, da wani tsarin da zai haɗe kansu, da wani jagoran da zai kare su, manzanni - amincin ya tabbata a gare su - sun jiɓinci hakan da Wahayi daga Allah - tsarki ya tabbatar maSa - suna shiryar da mutane zuwa hanyar alheri da shiriya, kuma ya haɗa su akan shari'ar Allah, suna hukunci da gaskiya a tsakaninsu, sai al'amuransu su daidaita gwargwadan amsawarsu ga waɗan nan manzannin, da kuma kusancin zamaninsu daga sakon nin Allah, kuma Allah Ya cika sakon ni da sakon manzo Muhammad - tsira da amincin Allah su tbbata agare shi -, kuma Ya rubuta mata wanzuwa ya sanyata shiriya ga mutane da rahama da haske da shiryarwa zuwa hanya mai sadarwa zuwa gareShi - tsarki ya tabbatar maSa -.

45. Saboda haka ina kiranka ya kai ɗan Adam ka tsaya ga Allah tsayuwa ta gaskiya kana mai tsiraita kanka daga kwaikwayo da al'ada, ka sani cewa kai bayan mutuwar ka zaka koma ne zuwa ga Ubangijinka, kuma ka kalli kanka, da wasu sassa da suke kewaye da kai, ka miƙa wuya zaka rabauta a duniyarka da lahirarka, idan kana son shiga musulunci babu abinda zaka yi sai kawai ka shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, kuma cewa (annabi) Muhammad manzon Allah ne, kuma kayi watsi da duk abinda ake bautawa koma bayan Allah, kuma kayi imani cewa Allah zai tashi waɗan da ke cikin ƙabari kuma cewa

hisabi da sakamako gaskiya ne, to idan ka shaida da Wannan Shaidawar to haqiqa ka zama Musulmi, saboda haka bayan haka zaka bautawa Allah da abunda ya Shar'anta na Sallah da Zakka da Azumi, da kuma Hajjatar Xakin Allah idan ka samu Iko yin hakan,

# Teburin bayani

MUSULUNCI.....................................................................2
Taƙaitaccen saƙo game da Musulunci kamar yadda yazo cikin Al-Kur'ani da Sunnanr Annabi.........................................................2

ha271v1.0 - 03/09/2026